صبح بہاراں



# SAFIYAR ALKHAIRAI صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

## (Hausa)


Shehun Darika Jagoran Ahlussunnah
Mahassasin Kungiyar Dawatul Islami Masani Maulana Abu Bilal

**MUHAMMAD ILYAS**

**Attar Qadiri Razavi**


Fassarar Hausa
Daga Shashen Fassara
Na Dawat-ul-Islam

صُبحِ بہاراں

Subh-e-Baharan

# SAFIYAR ALKHAIRAI

Wannan littafi mai albarka da Sheikhul Darika Jagoran Ahlussunnah wanda kuma shi ne ya kafa tubalin assasa wannan kungiya mai suna Dawatul Islami, wato Masani Maulana Abu Bilal Muhammad Ilyas Attar Kadiri Razavi دَامَتۡ بَرَکَاتُہُمُ الۡعَالِیَہ. **Translation Department** (Bangaren dake kula da fassara) ita ke da alhakin daukar nauyin fassarar wannan littafi zuwa harshen Hausa. Idan har an sami wani kuskure da ka iya aukuwa wajen fassara ko hadawa, muna roko da a gaggauta sanar da wannan Bangare dake kula da fassarar ta wannan adireshin akwatin gidan waya (postal address) ko kuma email address, da nufin samun lada [Sawab] daga Ubangij Maidaukaki.

**Translation Department (Dawat-e-Islami)**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagran, Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**UAN:** ☎ +92-21-111-25-26-92 – Ext. 7213

**Email:** 🖃 translation@dawateislami.net

**Safiyar Alkhairai**

Fassarar Hausa na Litafin'Subh-e-Baharan'

◆

## DUKKANIN HAKKOKI

Hakkin Mallaka © 2020 Maktaba-tul-Madinah

Ba'a yarda a yi kofin wannan littafi ba ko wani bangare nashi ta hanyar juya shi izuwa kowace irin siga misali kamar rubutun da ake bugawa ko akasin hakan (kamar dai rubutu a cikin na'ura mai kwakwalwa da sauran na'urori). Koma dai ta wasu hanyoyi daban da ba wadannan ba, har sai idan an samu izinin Maktabatul Madinah akan yiwuwar aikata hakan.

**Bugu Na Biyu:** Jumadal Aula, 1444 AH – (Dec, 2022)

**Masu Daukar Nauyin Bugawa:** Maktaba-tul-Madinah

**Quantity:** -

### DAUKAR NAUYI

Ga duk wanda ke da bukatar daukar nauyin buga wani adadi na kofin littafan addini domin yin sadakatul jariyyah ga wani mamaci da aka rasa, na iya tuntubar mu ta adiresinmu dake kasa.

**Maktaba-tul-Madinah**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah Mahallah Saudagran,
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**Email:** global@maktabatulmadinah.com | feedback@maktabatulmadinah.com

**Phone:** +92-21-34921389-93

**Web:** www.dawateislami.net | www.maktabatulmadinah.com

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَالصَّلٰوةُ وَالسَّلَامُ عَلٰى سَيِّدِ الْمُرْسَلِيْنَ

اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ ؕ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ ؕ

# Du’a for Reading the Book

Karanta wannan addu’a kafin fara nazarin littafin da ya shafi addini ko kuma daukar darasi na addinin Musulunci, domin hakan zai taimaka matuka wajen rikewa da fahimtar ilimin da aka nazarta, اِنْ شَآءَاللّٰه (cikin yardarm Allah Mai Girma da Daukaka):

اَللّٰهُمَّ افْتَحْ عَلَيْنَا حِكْمَتَكَ وَانْشُرْ
عَلَيْنَا رَحْمَتَكَ يَا ذَا الْجَلَالِ وَالْاِكْرَام

## Fassara

**Ya Ubangiji عَزَّوَجَلَّ! Muna rokon Ka da Ka bude mana kofofin (fahimtar) ilimi da hikima (daga gare Ka), kuma Ka rahamshe mu! Ya Mafi Daukaka da Karamchi!**

*(Al-Mustatraf, vol. 1, pp. 40)*

**Abin Lura:** Yi salati ga Annabi ﷺ (tsira da amincin Allah su tabbata a gare Shi) sau dai-dai kafin da bayan karanta wannan addu’a da aka gabatar a sama.

# Abubuwan da littafin ya kunsa


SAFIYAR ALKHAIRAI.......................................................................1
Falalar Salatin Ga Annabi ﷺ.......................................................1
Safiyar Alkhairai.........................................................................2
Baiwa.........................................................................................3
Daren da ya Dara na Lailatul Kadri ...............................................4
Idin Idodi ....................................................................................5
Abu-Lahab da Mauludi.................................................................5
Musulmai da Mauludi...................................................................6
Yi Murnar Mauludi Cikin Shauki ...................................................7
Annabi Tsarkakakke ﷺ Na Farin ciki da masu Nuna Farin Cikin HaihuwarSa ...................................................................................8
Daga Tutoti a Cikin Ayarin............................................................9
Iyalandake Gudanarda da Bikin Mauludi ........................................9
Ladan da ake Samun a Wajen Mauludi .........................................13
Yahudawa sun Rungumi Musulunci ............................................14
Kungiyar Dawat-ul-Islami Yayin Murnar Bikin Mauludi..................16
1. Waraka daga Aikin Sabo .........................................................17
2. Dattin Zuciya ya Fice ..............................................................18
3. Ruwan Annuri (Haske).............................................................20
4. Wani Zai iya Ganin Annabi Ko a Yau..........................................22
Ka’idodin Madani Guda 12 Na Yin Bikin Mauludi.............................24
Wasikar Attar akan Murnar Bikin Mauludi ......................................30
Gargadi......................................................................................34
Niyya Akan Gudanarda Bikin Mauludi............................................42
Niyyoyi 18 Domin Gudanar da Murnar Mauljudi ..............................44




www.dawateislami.net

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَالصَّلٰوةُ وَالسَّلَامُ عَلٰى سَيِّدِ الْمُرْسَلِيْنَ

اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ ؕ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ ؕ

# SAFIYAR ALKHAIRAI

## Falalar Salatin Ga Annabi ﷺ

Hakika Annabin da aka aiko zuwa ga talikai, Wanda Ya kasance (kwanciyar rai) nutsuwa ga zukatanmu, kuma mafi karamci da kyautayi (kirki) صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya fada cewa, 'Allah عَزَّوَجَلَّ Yana ba da lada har dari (rubanyawa izuwa ninki goma) ga dukkan wanda ya yi salati goma a gare Ni.' *(Al-Mu'jam-ul'l-Awsat lit-Tabarani, littafi na 5, shafi na 252, Hadisi na 7235)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Da zarar watan Rabi'ul Auwal (Watan Haske) ya gabato za ka ga kyakkyawan yanayi mai dadi tare da sanya annashuwa cikin yanayi mai ban sha'awa na wanzuwa a cikin dukkanin al'ummah. Mabiya Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم suna kasancewa cikin murna da zakuwa. Ga alamu dai dukkan Musulmi na kwarai namiji da mace, babba da yaro na bayyana tsantsar farin cikinsa da zuwan wannan wata mai albarka:

*Nisar tayri chahal pahal per hazar Eidayn Rabi'-ul-Awwal*
*Siwaye Iblees kay jahan mayn sabhi to khushiyan mana rahay hayn*



www.dawateislami.net

Yayinda duhun kafirci da bautar gumaka ya game duniya, wani haske ya bayyana a tsarkakakken dakin Sayyidatuna Aaminah رَضِیَ اللہُ عَنۡہَا (Allah Madaukakin Sarki Ya kara yarda a gare Ta), a cikin garin Makkah abar karramawa, wanda ya haskaka dukkanin duniyya. Annabin Rahama صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Wanda dukkanin al'ummar duniya da suka wanzu cikin dimuwa da rudani ke zaman jira cikin zakuwa, Ya bayyana tare da alkhairai masu dumbin yawa ga dukkan duniyya.

*Mubarak ho kay Khatm-ul-Mursaleen tashreef lay aaye*
*Janab-e-Rahmat-ul-lil-'Aalameen tashreef lay aaye*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب          صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Safiyar Alkhairai

Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, Ya iso duniyya ranar sha biyu (12) ga watan Rabi'ul Auwal (Watan Haske) a tsakiyar dare tare da sauya bakin daren da ya kasance cike da rudani, wahalhalu, masifu da bala'o'i izuwa ga farar safiya mai cike da farin ciki da walwala.

*Musalmano Subh-e-Baharan mubarak*
*Woh barsaatay anwaar Sarkar* صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم *aaye*

*(Wasail-e-Bakhshish (amended), pp. 499)*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب          صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Baiwa

Da isowar Hasken Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم duniya ranar 12 ga watan Rabi'ul Auwal, sai bakin duhun guguwar zalunci da kafirci ya gushe. A daya bangare kuwa fadar sarkin Kisra, wadda ta kasance mallaki ga sarkin daular Iran, ta girgiza har ta kai ga faduwar sha hudu (14) na gumakansu, tare da mutuwar wutar da ta kasance tana ci tsahon shekaru dubu gabanin zuwan wannan dare mai albarka, a wannan nahiya dai ta Iran. Koramar 'Saba' ma da kanta ta kafe yayin da dakin Ka'abah shi ma ya girgiza har gumakan dake ciki suka fadi akan fuskokinsu.

*Tayri aamad thi kay Baytullah mujray ko jhuka*
*Tayri haybat thi kay her but thar thara ker gir gaya*

*(Hadaiq-e-Bakhshish, pp. 41)*

*Ka'abah ta girgiza yayin zuwanSa*
*Gumakan sun fadi suna masu mirginawa cikin kaduwa*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Babu shakka Annabin Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya sauko a matsayin rahama kuma ranar saukar rahamar Allah عَزَّوَجَلَّ hakika ranar murna da farin ciki ce. Allah عَزَّوَجَلَّ Ya fada a cikin Al-Qurani Tsarkakakke cikin Surah ta 11, Suratul Yunus, Aya ta 58 cewa:

قُلْ بِفَضْلِ اللّٰهِ وَ بِرَحْمَتِهٖ فَبِذٰلِكَ فَلْيَفْرَحُوْا ؕ هُوَ خَيْرٌ مِّمَّا يَجْمَعُوْنَ ﴿۵۸﴾

*Ka ce, 'Da (Kawai) falalar Allah da rahamarSa. Sai su yi farin ciki da wannan. Shi ne mafi alheri daga abinda suke aikatawa.*

*[Kanz-ul-Iman (translation of Quran)] (Part 11, Surah Yunus, verse 58)*

اَللّٰهُ اَكْبَر! (Allah Mai Girma), Al-Qur'ani da Kansa ya yi umarni da yin murna da nuna farin ciki a bisa wata rahama da ta wanzu a tsakaninmu, kuma mafi girman rahama da Allah Ya saukar ta tattaru ne ga zuwan Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, kaman yanda aka bayyana karara a cikin Al-Qur'ani Mai Tsarki, Surah ta 21, Suratul Anbiya, Aya ta 107:

وَ مَاۤ اَرْسَلْنٰكَ اِلَّا رَحْمَةً لِّلْعٰلَمِيْنَ ﴿۱۰۷﴾

*Kuma ba Mu aike ka ba face domin wata rahama ga talikai.*

*[Kanz-ul-Iɴan (Fassarar Al-Qura'ani)] (Surah ta 21, Suratul Anbiya, Ayata 107)*

## Daren da ya Dara na Lailatul Kadri

Shugabana Sheik Abdul Haq Muhaddis Dihlivi رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya fadi cewa, 'Tabbas daren haihuwar Annabinmu abin kauna kuma mai albarka صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yafi daren Shab-e-Qadr (Lailatul Kadri),

wanda ya kasance daya daga cikin darare da aka gadar a matsayin kyauta ta ban girma ga Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. A hakikanin gaskiya dai, daren da darajarsa ta rataya bisa ga zuwan Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya wuce darajar daren da darajarsa ta rataya akan saukowar mala'iku.

*(Masabata bis-Sunnah, shafi na 100)*

## Idin Idodi

اَلْحَمْدُ لِلّٰه! Shakka babu Sha-biyu (12) ga watan Rabi'ul Auwal (Watan Haske) ranar Idi ce da ta zarce dukkan Idodi ga dukkan Musulmi. Tabbas ba dan zuwan Annabi Tsarkakakke, صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم duniyya ba, da ba'a halarci wata Idi ba kuma ba'a rabauta da *Shab-e-bara'at* (Daren Gafara, Darendake tsakanin 14 da 15 ga watan Sha'aban) ba. Hakika dukkannin darajoji da daukaka na duniyya da lahira sun samo asali ne daga zuwan Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم wannan duniya.

*Woh jo na thay to kuch na tha woh jo na haun to kuch na ho*

*Jan hayn woh jahan ki, jan hay to jahan hay*

*(Hadaiq-e-Bakhshish, pp. 126)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Abu-Lahab da Mauludi

Wasu daga cikin iyalai ga Abu Lahab sun yi mafarkinsa a yanayi na kangi bayan mutuwarsa. Yayinda suka tambaye shi

shin ko yaya ya sami kansa bayan mutuwa sai ya ce, 'Ban riski wani alkhairi ba bayan barin ku.' Sa'annan ya kara da cewa, yayin da yake nuni da ramin dake karkashin Babban dan yatsansa, 'idan ka dauke wannan, domin an kasance ana shayar dani ruwa daga wannan rami sakamakon yanta kuyangata (baiwa) Suwaibah.' *(Musannaf 'Abdur Razzaq, littafi na 9, shafi na 9, Hadisi na 16661'; 'Umda-tul-Qaari, littafi na 14, shafi na 44, Hadisi na 5101)*

Sheik Masani (Allamah) Badruddin AYni رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه ya fadi cewa: 'Wannan alama ce ta cewa ana ba shi (Abu Lahab) ruwa.'

*('Umda-tul-Qaari, littafi 14, shafi na 44, Hadisi na 5101)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Musulmai da Mauludi

Shugabana Sheik Abdul Haq yayin da yake tsokaci akan wannan labari da ya gabata, ya fada cewa: 'A cikin wannan lamari (na baiwa Abu-Lahab ruwa) akwai cikakkiyar hujja ga masu nuna farin ciki da murnar zuwan Annabi Mai Daraja صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم tare da yin hidima da dukiya a ranar wannan taro mai dunbin alkhairai. Idan Abu-Lahab wanda ya kasance rikakken kafiri ya amfana domin nuna farin ciki da ya yi ta hanyar yanta kuyangarsa Suwaibah yayin da ya ji albishir na haihuwar Annabi Mai Daraja صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Toh wane irin dumbin alkhairai kuma Musulmin da ya kashe dukiyarsa da zuciya daya, domin nuna farin ciki da irin wannan taro na



www.dawateislami.net

murnar zuwan Annabin Rahama صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم duniyya zai ribata kenan. Duk da haka dai ya zama wajibi a kauracewa wake-wake da kide-kide a dukkanin tarukan mauludi.'

*(Madarij-un-Nubuwwah, Littafi 2, shafi na. 19)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب      صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Yi Murnar Mauludi Cikin Shauki

Ya ku yan'uwa Musulmi! Ku bayyana murna da haihuwa mai albarka ta Annabi Tsarkakakke, صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم cikin shauki. Ku sani cewa har fa rikakken kafiri kamar Abu-Lahab ya amfana da nuna farin ciki akan haihuwar Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Idan ko hakane toh kuwa babu ko shakka cewa tabbas mu Musulmi mun fi kowa kusanci tare da cancantar samun wannan kabakin alkhairai. Abu-Lahabi dai murna kawai ya yi da haihuwar Dan Dan'uwansa maimakon (amma fa ba) murnar zuwan Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, amma fa duk da haka alkhairin wannan aiki (ya wanzu a gare shi) bai tsallake shi ba. Toh ta yaya mu kuma (Musulmi) za mu kasa rabauta da lada yayin aiwatar da bikin murnar zuwan Fiyayyn Halittata صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم duniyya, cikin soyayya da kauna?

*Ghar Aaminah kay Sayyid-e-Abrar aa gaya*
*Khushiyan manao Ghamzado Ghamkhuwar aa gaya*

*Sarkin Annabawa ya sauka gidan Aaminah*
*Yi murna, Ya kai mai dumbin bakin ciki, Maganin bakin cikinka ya iso*
*(Wasail-e-Bakhshish, shafi na. 474)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Annabi Tsarkakakke ﷺ Na Farin ciki da masu Nuna Farin Cikin HaihuwarSa

Wani malamin Addinin Musulunci ya fadi cewa ya ga Annabin talikai صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, Wanda Ya kasance kwanciyar rai da nutsuwar ga zukatanmu, kuma mafi karamci da kyautayi (kirki), a cikin mafarkinshi har ya tambaya Shi da cewa, 'Ya Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, Ko Kana farin ciki da Musulmin dake nuna farin ciki da haihuwar Ka?' Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya amsa masa da cewa, 'Ina farin ciki da wanda ke farin ciki da Ni.' *(Tazkira-tul-Wa'izeen, pp. 125)*

## Matsayin Sanya Tutoci Yayin Bikin Mauludi

Sayyidatuna Aaminah رَضِىَ اللّٰهُ عَنْهَا (Allah Ya Yarda da Ita) ta fadi cewa: 'Yayin da Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya iso duniyya, Na ga tutoci guda uku a kafe; daya a gabas, daya a yamma yayinda daya kuma ke saman rufin Ka'abah.' *(Khasaais-ul-Kubra, littafi na 1, shafi na 82)*

*Ruh-ul-Ameen nay gaara Ka'bay ki chat pay jhanda*
*Ta 'Arsh ura pharayra subh-e-shab-e-wiladat*

*Amintaccen Ruhi Ya kafa tuta a saman rufin Ka'abah wadda ta daga izuwa sama a safiyar alkhairai*

*(Zauq-e-Na'at, pp. 95)*

## Daga Tutoti a Cikin Ayarin

Yayin Hijira izuwa Madina (Munawwarah), a lokacin da Abin Kauna Annabi Mai albarka صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya isa wani bagire dake daf da Madina (Munauwarah), da ake kira da suna Mauda'-e-Ghameem, Buraidah Aslami tare da rundunarsa ta mutun saba'in mahaya dawakai, daga kabilar Bani Sahm, sun bi sawun matafiyan da nufin cimma Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, amma shi ma da kansa sai ya kamu da soyayyar Manzo Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم kuma nan take ya rungumi Addinin Musulunci. Bayan kasancewar hakan nan take sai ya ce: 'Ya Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم! Za mu kasance daga cikin jerin masu taryar Ka a garin Madina (Munauwarah) yayin da muke rike da totoci.' Sabida haka take mahaya dawakan dake tare da shi suka cire rawunansu tare da sanya su a saman masun su kuma suka wuce gaba izuwa garin Madina (Munawwara). *(Wafa-ul-Wafa, littafi na. 1, shafi na 243)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Iyalandake Gudanarda da Bikin Mauludi

An yi wani bawan Allah mai tsoron Allah عَزَّوَجَلَّ da ake kira Ibrahim dake zaune a garin Madina (Munauwrah). Ya kasance

cikakken Mabiyin Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم kuma mutum mai neman halak dinsa domin gudanar da al'amuran rayuwarsa na yau da kullun. Amma hakan bai hanashi tanadin Mauludi ba domin kuwa kullun ya kan ajje rabin abinda ya samu domin dai ya tanadi wannan lokaci na yin murnar ranar haihuwar Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Ta yanda yayin da watan Rabi'ul Auwal ya zagayo zai yi amfani da wannan tanadi nasa wajen aiwatar da bikin mauludi cikin tsananin shauki da annashuwa tare da kokarin ganin ya tsaya akan iyakokin Shari'ah (ba tare da ya keta su ba). Ya kan raba abinci mai yawa tsakanin mutane domin aika ladan ga Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم kuma domin ya tabbatar cewa ya kashe dukiyarsa ne ta hanyar Allah. Kamar dai shi, haka ma matarsa ta kasance mai hidima matuka ga Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Domin ta na ba da goyon baya ga mijinta matuka a cikin aiwatar da wannan aikin alkhairi.

Bayan shekaru kadan sai wata rana kwatsam sai Ibrahim ya kira dansa tare da bar mishi wasiya cewa, 'Ya dana, zan koma ga Allah عَزَّوَجَلَّ a daren yau. Na bar dirhami 50 da yadi 19 na tufafi. Yi amfani da yadin wajen yi min sutura (likkafani), sa'annan kudin kuma ka kashe su ta yanda ka so muddin dai ta hanyar aikin kwarai ne.' Bayan fadin haka sai ya karanto shikashikan imani (kalmar shahada) daga nan ya cika. Hakanan dai dan nasa ya binne shi kamar yadda ya umarce shi amma sai ya shiga rudani akan ta yanda zai kashe kudin da mahaifinsa ya bari. Bayan ya yi bacci a daren wannan rana sai ya yi mafarkin cewa an tashi Alkiyama kowa a firgice. Mutanen

da suka rabauta na tafiya izuwa ga Aljannah, yayin da ake jan tababbu izuwa gidan wuta. Shi dai yana tsaye cikin firgici da rawar jiki bisa fargabar inda makomarsa za ta kasance. Ana cikin haka kawai sai aka ba da sanarwa cewa. 'Ku bar wannan matashin ya wuce Aljannah.'

Sabida haka ya shiga Aljannah cikin farin ciki ya yi ta yawo ba tare da wata fargaba ba amma bayan ya shiga Aljannah ta shida har ya kai gabar da zai shiga izuwa Aljannah ta bakwai sai aka ce mishi ya Dakata domin wadanda suka yi murnar zuwan Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ne kadai ke shiga wannan Aljannah. Da jin haka sai ya yi hasashen cewa tabbas mahaifansa suna cikin wannan Aljannah. Kwatsam sai ga wata murya tana sanarwa cawa, 'Ku bar wannan matashin ya shige domin mahaifansa na so su gana da shi. Sabida haka sai ya shiga, a inda ya tarar da mahaifiyarsa zaune kusa da wata korama daga kogin Kausara. A kusa da ita ga wata kujrar mulki dauke da wata mace mai daraja. Ga kuma wasu kananan kujeru nan dake dauke da wasu mataye masu daraja dake zaune bisansu. Take kuwa sai ya tambayi wani mala'ika cewa: 'Shin su waye wadannan?' Aiko mala'ikan nan sai ya amsa masa da cewa: 'Wadda ke zaun kan kujerar Mulki, Sayyidatuna Fadimah Zahra kenan, yayin da sauran matayen dake kan kujeru sune: Sayyidatuna Khadijatul Kubra, Sayyidatuna 'Aishah Siddiqah, Sayyidatuna Maryam, Sayyidatuna Aasiyah, Sayyidatuna Saarah, Sayyidatuna Haajirah, Sayyidatuna Raabi'ah da kuma Sayyidatuna Zubaida رَضِیَ اللهُ عَنْهُنَّ (Allah Madaukakin Sarki Ya kara yarda da Su).



www.dawateislami.net

Nan take farin ciki ya dada lullube shi kuma ya cigaba da tafiya wanda hakan ya sanya idanuwansa cin karo da wani mashahurin al'amari dake matukar karfafa Imanin dan Adam. Yayin da ya tsinkayi wata gawurtacciyar kujerar mulki wadda Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ke zaune akan ta. Gewaye da Shi kuma ga wasu karin kujeru hudu dauke da Khulafa' ul rashidin (Khalifofin nan guda hudu ingantattu رَضِىَ اللهُ عَنْهُم). A bangaren dama kuwa wasu kujerun gwala gwalai ne reras dauke da Annabawan Allah عَلَيْهِمُ الصَّلٰوةُ وَالسَّلَام (tsira da aminci ya tabbata a gare Su), yayin da kuma daga bangarn hagu Shahidai ne ke zaune tare da Ma'aiki. Nan take dai wannan matashi ya hango mahaifinsa Ibrahim a cikin dandazon dake kusa da Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Nan dai Ibrahim ya rungume dansa cikin matukar farin ciki. Bayan Dan ya tambayi Ibrahim cewa: 'Ya mahaifina, taya ka yi ka riski wannan matsayin mai girma?' Sai Ibrahim ya amsa masa da cewa: 'اَلْحَمْدُ لِلّٰه (Na godewa Allah عَزَّوَجَلَّ), na riski wannan matsayi ne ta hanyar yin murna da zuwan Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم duniyya.'

Da wayewar gari kuwa matashin nan (wato da ga Ibrahim) ya siyar da gidansa tare da shirya liyafa ta hanyar amfani da wannan kudi na gida hade da kudin da mahaifinsa ya bar masa wato dirhami hamsin (50). A inda ya tara malaman addinin musulunci tare da wasu Musulmi masu tsantseni da tsoron Allah ya kuma hidimta musu ta hanyar ciyarwa. In takaice maka zance dai, a wannan safiya wannan duniyyar ta fice daga ran wannan matashi domin har ta kai ga ya yanke shawarar

tarewa a masallaci domin karar da sauran shekarunsa. A haka dai ya karar da sauran shekarunsa talatin da suka rag masa cikin bautar Allah عَزَّوَجَلَّ.

Bayan rasuwarsa wani bawan Allah ya gan shi cikin mafarki har ya tambaye cwa shin me ya faru gare shi bayan mutuwa. Sai ya amsa cewa: Sakamakon alkhairan dake cikin nuna farin cikin Mauludi, na sami matsayi irin wanda mahaifina ya samu a cikin gidan Aljannah.' *(Tazkira-tul-Wa'izeen, shafi na 557)*

*Bakhsh day mujh ko Ilahi! Bahr-e-Milad-un-Nabi*
*Naamah-e-a'maal 'isyan say mayra bharpoor hay*

*(Wasail-e-Bakhshish (amended), pp. 484)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Ladan da ake Samun a Wajen Mauludi

Sheik Abdul Haq Muhaddis Dihlivi رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه ya ce, 'Wadanada suke nuna farin cikinsu a daren haihuwar Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم za su shiga Jannatun-Na'im, cikin rahamar Allah عَزَّوَجَلَّ. Musulmai sun wanzu suna masu murnar haihuwar Masoyi Annabi Mai albarka صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ta hanyar girka abinci kala kala tare da gayyatar al'ummah da kuma ba da sadaka mai yawa. Sun kasance masu bayyana farin cikinsu ta hanyar sadaukar da dukiyoyinsu cikin dadin rai, tare da tara jama'a duk domin dai bikin murnar haihuwar Tsarkakakken Annabi

صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Sa'annan kuma dai sukan kawata gidajensu da ado yayin da a daya bangare kuma Allah Ubangiji ne da KanSa عَزَّوَجَلَّ ke saukar da alkhairanSa da rahamarSa a gare su sakamakon wannan kyakkyawan aiki nasu (na bayinSa). *(Masabata bis-Sunnah, shafi na 102)*

## Yahudawa sun Rungumi Musulunci

Shugabana Abdul Waahid Bin Isma'eel رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه ya rawaito cewa: 'Wani Babban mabiyi kuma hadimi ga Annabi ya rayu a Kasar Egypt. Wannan bawan Allah ya kasance yana gudanar da bikin murnar haihuwar Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم cikin matukar zakuwa da annashuwa. Sai kuma ya kasance cewa ya yi makwabtaka da wasu iyalai yahudawa. Toh Kasancewar a duk sa'adda watan Rabi'ul-Auwal ya shigo, Bayahudiyar matar kan tambayi mijinta cewa: 'Meyasa Musulmin nan Makwabcinmu ke shirya wannan gagarumar liyafa a cikin wannan watan da muke ciki.' Sai mijin nata ya amsa mata da cewa, 'A wannan watan aka haifi Annabinsa صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, sabida haka yana gudanar da wannan hidima ne domin murnar haihuwar Annabinsa صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, kuma musulmai suna girmama wannan wata matukar girmamawa.' Bayan jin haka daga gare shi sai ta kada baki ta ce, 'Abu ne mai kyau da Musulmi ke yin murnar haihuwar Annabinsu صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم a duk shekara.'

Bayan wannan Bayahudiya ta yi bacci a wani dare (bayan irin wannan hira ta wakana tsakanin ta da mijinta) sai ta yi mafarki da Wani Tsarkakakken Mutun Mai girma da cikar zati, na

haskakawa cikin wani dandazon jama'a dake kewaye da Shi. Sai ta matsa kusa inda ta tambayi wani a cikin mutanen dake wannan waje akan cewa Shi kuma Wannan Madaukakin Mutun Mai daraja ko Waye ne. Mutumin ya amsa mata da cewa, 'Shi ne cikamakin Annabawa (Annabin Karshe) صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Ya iso ne domin ganawa tare da sanyawa makwabcinku albarka sakamakon aikinsa na gudanar da bikin murnar haihuwarSa.' Sai Bayahudiyar ta kara tambaya a karo na biyu, 'Ko zai min magana?' Mutumin nan dai ya kara amsa mata da cewa, 'Eh.' Take sai matar ta yi kira izuwa ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Shi kuwa Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم da jin haka sai Ya amsa mata, wanda hakan ya yi matukar burge ta ganin cewa Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya amsa mata kiranta, wanda hakan kuma ya sa ta ce da Shi a karo na biyu, 'ni ba musulma ba ce amma duk da haka ga shi Ka amsa min.' Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم sai Ya ce, 'Allah عَزَّوَجَلَّ Ya shaida Min cewa za ki karbi Musulunci nan ba da dadewa ba.' Daga jin haka sai ta yi zunbur ta ce: 'Babu shakka Kai kam Rahama ne ga dukkan al'ummahh kuma Annabi abin girmamawa, duk wanda ya saba maKa ba zai taba cin nasara ba kuma wanda duk ya ki yarda da girman matsayinKa tabbas zai wanzu cikin asara. Sannan sai ta karanta kalimar shahada.

Yayin da ta farka sai ta tashi tana mai rungumar addinin Musulunci tare da dukkan zuciyarta. Take kuwa ta kulla niyyar kashe dukkan tanadinta wajen bikin murnar haihuwar Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ta hanyar ba da abinci ga mutane da wannan safiya. Ga mamakinta sai ta tarar da mijinta na ta

faman hada gagarumar liyafa. Sai kuwa ta tambaye shi cikin mamaki cewa: 'Me kake aiwatawa ne haka? 'Sai ya amsa mata da cewa: 'Ina hada abinci ne domin nuna murnar shigarki addinin Musulunci.' Da jin haka sai ta kara tambayar sa cewa: 'Amma ta yaya ka san haka?' Shi kuwa sai ya amsa mata da cewa: 'Kaman dai ke, nima na ga Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم a daren jiya cikin mafarki kuma nima na rungumi addinin Musulunci.' *(Tazkira-tul-Wa'izeen, shafi na 598)*

Allah عَزَّوَجَلَّ Ya yi rahama a gare su mu kuma Ya yafe mana ba tare da tuhumaba sabida albarkacin wadannan bayin nashi na kwarai!

اٰمِيْن بِجَاهِ خَاتَمِ النَّبِيّٖن صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

*Aamad-e-Sarkar say zulmat huyi kafoor hay*
*Kya zameen, kya aasman her samt chaaya Noor hay*

*ZuwanSa ya cire duhu daga ko'ina*
*Haske ya wanzu daga doron duniyya izuwa ga sama'u gaba daya*
*(Wasail-e-Bakhshish (amended), pp. 483)*

## Kungiyar Dawat-ul-Islami Yayin Murnar Bikin Mauludi

اَلْحَمْدُ لِلّٰه, (Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Mai Girma da Daukaka) Dawatul Islami wadda ta kansance kungiya ta duniyya dake barranta daga harkokin siyasa, wadda kuma aka assasa domin yada ilimin Al-Qur'ani (Mai Girma) da Sunnar Ma'aiki صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ta kasance tana da sahihiyar hanya ta

musamman da take amfani da ita wajen gudanar da murnar bikin Mauludi. Wannan kungiya kan tara tarukan Mauludi na dandazon mutane masu tarin yawa a kasashe daban daban na duniyya. Ga dukkan alamu dai mafi girman taron Mauludi a duniyyaya na faruwa ne a garin Karachi dake Kasar Pakistan a kowace shekara. Wadannan taruka sun kasance wasu daga cikin gawurtattun tarukan addini da suka karfafi Kungiyar Madani a kokarinta na gudanar da juyin juya hali da nufin ganin cewa ta sauya yanayin rayuwar dubban mutane da suka kasance cikin ayyukan sabo, domin juyewa izuwa mabiya sunnar Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم tsantsa. Karanta hudu daga cikin fitattun nasarorin Madani a wannan bangare, kaman yanda suka zo a kasa.

## 1. Waraka daga Aikin Sabo

Wani hadimi ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya bayyana a mauludin Nabi (1426 AH) cewa: ’Wani abokina da ya kasance mai matukar son kawace kawace na duniyya tare da rashin guganar da sallah, ya halarci taron Mauludi da aka gudanar a Filin Kakri dake Bab-ul-Madinah a cikin garin Karachi. A lokacin da ake gaisuwar Subh-e-Baharan (Safiyar Alkhairai), yayinda kowa ya kasance yana karanta salati da gaisuwa ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, Sai hakan ya yi matukar burge abokina kuma har ya ji cewa tsanar aikin sabo ya shiga zuciyarsa inda daga nan ya daura cikakkiyar niyyar tsayar da sallah tare da ajje gemu. اَلْحَمْدُ لِلّٰه, (Allah عَزَّوَجَلَّ abin godiya), wannan bawan Allah عَزَّوَجَلَّ ya

cika niyyarsa ta tsaida sallah har ma da ajje gemu. Hakika kuma ya kasance yana da wata munmunar dabi'a wadda bai kamata a bayyana ta ba amma dai sakamakon halartar wannan taro mai albarka Allah عَزَّوَجَلَّ Ya raba shi da ita wabban dabi'a ko cuta. A takaice dai wannan bawan Allah da ya kasance yana fama da muguwar cuta dake sanya shi aikata aikin sabo ya sami waraka ingatacciya.

*Maang lo maang lo un ka gham maang lo*
*Chashm-e-rahmat nigah-e-karam maang lo*

*Ma'siyat ki dawa la-jaram maang lo*
*Maangnay ka maza aaj ki raat hay*

*Roki rahamarSa da alkhairanSa a wannan dare mai tsarki*
*Roki kariya daga aikin sabo a wannan dare mai tsarki*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## 2. Dattin Zuciya ya Fice

Labari ya zo mana a rubuce daga wani dan'uwa Musulmi dake Arewacin garin Karachi wanda ke cewa: 'A farkon watan Rabi'ul Auwal wasu masu hidima kuma mabiya ga Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم da suka kasance suna masu hada kudi a karan kansu domin wannan hidima, sun gayyace ni taron Mauludi da ya gabata a farfajiyar Kakri, Bab-ul-Madina dake garin Karachi. Na kasance mai matukar sa'a bayan da na amsa tare



www.dawateislami.net

da tabbatar musu cewa zan zama daya daga cikin masu ba da gudunmawarsu a wajen gudanar da wannan taro. Ai kuwa na cika alkawarina a daren 12 ga watan Rabi'ul Auwal kamar yadda na dauka a inda na kasance zaune a cikin doguwar motar bos (bus) tare da dukkanin sauran yan'uwa musulmi, akan haryarmu ta tafiya izuwa ga wannan taron mauludin. Abin sha'awa wani hadimi a cikin tafiyar ya kasance yana da wata alewa mai suna 'Cham Cham' inda ya karkasa ta wajen kashi talatin tare da raba ta dai-dai a tsakaninmu. Wannan lamari ya kayatar da ni matuka kasancewar sa lamari dake nuni da tsantsar kaunar juna. Hakanan dai al'amuranmu suka yi ta gudana har muka isa wannan wajen taron Mauludi mai albarka.

'Wannan shi ne karon farko a rayuwata da na ga irin wannan taron addini mafi burgewa. Amon sautin Na'at (Baitoci ga Annabi) da gaisuwa gare Shi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya game ko'ina da ina yayin da mutane ke ta faman rera wannan amshi cikin shauki da annashuwa, 'Marhaba Ya Mustafa,' ma'ana 'Maraba da zuwan Mustafa' صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.' Take sai na ji a raina tamkar shaukin wannan taro na cire min dukkan dattin zuciyata. اَلْحَمْدُ لِلّٰه (Na godewa Allah عَزَّوَجَلَّ), domin kuwa ba tare da daukar wani dogon lokaci ba cikin yardar Allah عَزَّوَجَلَّ na samu kaina a matsayin daya daga cikin 'ya'yan wannan kungiya ta Madani dake kira izuwa ga addinin Musulunci, wanda ya sanya yanzu haka nake sanya koren rawani kuma na ajje gemu domin koyi da Sunnar Ma'aiki صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. A yanzu haka ina ba da gudunmawata a matsayin 'Alaqa'ee Nigran (mai kulawa da



www.dawateislami.net

wani yanki) a wannan kungiya ta Dawatul islami a bangaren nan na yada sunnonin Ma'aiki صَلَّى اللهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*'Ata-e-Habib-e-Khuda Madani Mahaul*
*Hay fayzan-e-Ghaus-o-Raza Madani Mahaul*

*Yaqinan muqaddar ka woh hay sikandar*
*Jisay khayr say mil gaya Madani Mahaul*

*Majalisin Madani, falala daga Allah*
*Cikar kirkin Mai taimako da gamsuwar*
*zuciyarsa ita ce majalisin Madani*
*Hakika, mai sa'a shi ne wanda ya kasance*
*daya daga cikin jama'ar dake cikin majalisin Madani*
*(Wasail-e-Bakhshish (amended), pp. 646-647)*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## 3. Ruwan Annuri (Haske)

A taron bikin Mauludin Nabi صَلَّى اللهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم na shekarar 1417 A.H., tawagar Dawatul Isalami (Tsagen Nazimzbad, dake garin Karachi) sun kama haryar komawa izuwa gidajensu bayan sallar Azahar. Wannan tawaga ta kunshi tarin mahalarta wannan Mauludi masu dumbin yawa wadanda suka kasance suna nuna murna cikin annashuwa tare da rera baitoci kala kala cikin shauki. Tawagar dai ta samu tsayuwa a wajaje da

dama domin kira da kyakkyawan aiki. Kuma cikin Taimakon Allah عَزَّوَجَلَّ, a duk inda suka tsaya domin su yi kira sai kaga mutane na ba da hadin kai tare da saurare cikin nutsuwa. Bayan kammala bayanansu a wani bagire da suka samu tsayawa, nan take wani mutun ya yunkuro izuwa ga wannan masu kira, tare da shaida mu su cewa: 'Na ga wani haske da idanuna da ya kasance yana kwaranya akan duk wadanda ke wannan waje, yaro da babba (na mutanen dake gabatar da Kiran), yayin da kuke gabatar da wannan bayani. Ku yi hakuri kasancewar ni ba Musulmi bane amma ina so ku shigar dani addinin Musulunci yanzu ba tare da bata lokaci ba.' Nan take wadannan masu da'awa suka sake rera baitocin yabo cikin shauki. Hakika wannan ba karamin al'amari bane, ganin cewa har ta kai ga Shaidan da kansa ya rasa tasirinsa sakamakon daukakar da Allah عَزَّوَجَلَّ Ya azurta wannan tawaga ta Madani da ita, tare da sanya albarkarSa ga wannan Kungiya ta Dawatul Islami dake kira domin yada addinin Musulunci. Bayan wannan bawan Allah ya karbi musunci sai ya nufi gidansa domin baiwa iyalansa goron gayyata izuwa ga shigowa wannan addini mai albarka na Musulnci. Sakamakon karfin tasirin wannan kira nasa ga iyalansa ya sanya matarsa, yayansa guda uku tare da mahaifinsa, dukkanin su suka karbi addinin Musulunci.

*Eid Milad-un-Nabi hay dil bara masroor hay*
*Han magar Shaytan ma' rufaqa bara ranjoor hay*

*A Ranar Bikin Mauludin Nabi Kowa Na Kasancewa*
*Cikin Matukar Farin ciki da Shauki*
*Yayin da Shadan da Mukarrabansa ke wanzuwa*
*cikin bakin ciki da kasalar Jiki.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## 4. Wani Zai iya Ganin Annabi Ko a Yau

Wani hadimi kuma mabiyi ga Annanbi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya fada cewa: 'Mun halarci (mafi girman) taron Mauludi da majalisin Dawatul Islam ya gabatar a farfajiyar Kakri a Bab-ul-Madinah dake garin Karachi. Yayin tattaunawa wani dan'uwa Musulmi ya furta cewa, 'Taron Mauludi na Dawatul Islami ya kasance mai kayatarwa a baya sabanin yanzu da wannan tasiri nasa ya disashe.' Da jin haka sai wani dan'uwa daban a musulunci ya maida martani da cewa, 'A'a Abokina! Ba haka lamarin yake ba! Wannan taron har yau yana nan da tasirinsa na kayatarwa kamar yadda yake a baya. Ta yaya ka ke tunanin tasirin zikirin (ambaton) Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم zai taba canjawa? Ni ina ganin dai kawai zukatanmu da tunaninmu ne suka canja! Domin dai koda a yau din nan, da ace za mu kasance masu saurare ga Na'at (kasidodi) tare da kudircewa a zukatanmu cewa muna lullube cikin falalar da karamar Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, maimakon kokarin dulmiyar da kawunanmu a cikin bakin duhun rami na sukar juna da jayayya, aiko da tabbas mun sha

romon alkhairan dake cikin wannan taro إِنْ شَآءَاللّٰه (cikin yardar Allah عَزَّوَجَلَّ).' Ikirarin da dan'uwa Musulmi na farko ya yi tabbas ka iya karyawa mahalarta wannan taro gwiwa a cikin wannan aikin nasu na alkhairi har ta kai ga ya sanya wasu kama hanyar komawa gidajensu, sai dai kuma maganar dan'uwa Musulmi na biyu ta kasance akan hanya. Na dai takace muku zance, bayan karfafa mana gwiwa da wannan dan'uwa ya yi ni kam sai na zauna tsakanin mahidimtan ga Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم tare da fara sauraron kasidodin da suke rerawa, cikin shauki da soyuwa.

Yayinda hasken alfijir ya fara ketowa nan take sai dukkan yan'uwa Musulmi suka mike domin yin maraba da safiyar alkhairai. A daidai wannan lokaci kuma mahalarta wannan Mauludi mai albarka sun kasance cikin wani irin shauki mara misaltuwa. Sabida haka amon sautin kiran da muke ta yi 'Marhaba' (Maraba) ya cika wajen baki daya. Ana ta faman jero salati da gaisuwa ga Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم! Sai kwalla kawai kake gani na zuba daga idanuwan wadannan masoya ga Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Ga mutane na ta zubda hawaye ta kowace kusurwa dake wannan wajen.' Ni da kaina sai da na riski kaina cikin matukar shauki. Tabbas (sabida rahama ta Ubangiji) na gani da idanuwana masu aikata sabo yayin da wani dandazon ruwan kwayoyi (Kamar digon dusar kankara) ke sauka a wannan taro mai albarka. Nan take na rufe idanuwana tare da cigaba da kwararo salati da gaisuwa ga Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Ai kuwa nan da nan idanuwan zuciyata

suka bude sarai, yayin da na yi katarin ganin Wanda ake murnar wannan Mauludi domin Sa! Lallai kam yau na yi farin duba domin na yi katarin ganin Annabin Rahama Maceci ga Al'ummah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.'

اَلْحَمْدُ لِلّٰه! (Nagode Allah عَزَّوَجَلَّ) da Ya albarkaci zuciyata da samun nustuwa. Tabbas wannan dan'uwa Musulmi ya yi gaskiya da furta cewa taron Mauludi na Dawatul Islami yana nan da karsashinsa kaman kullun, sai dai zukatanmu ne kawai suka sauya, amma da za mu zama masu tara hankulanmu kan wannan taro, koda a yau wani zai iya ganin Masoyi Annabi Mai albarka صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.'

*Koi aaya pa kay chala gaya, koi 'Umar bhar bhi na pa saka*
*Yeh baray karam kay hayn fayslay, yeh baray naseeb ki baat hay*
*Wani ya zo ya samu nan da nan, yayinda wani ba zai taba samu ba -*
*wadannan hukunce hukunce ne na Ilahidake rubuce tun fi azal*

## Ka'idodin Madani Guda 12 Na Yin Bikin Mauludi

1. Kawata gidajanku, Masallaci, shaguna tare da ababan hawanku da kyallaye domin gabatar da bikin murnar haihuwar Annabin Rahama, Mai ceton al'ummah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Haskaka gidanka da a kalla gulab na kwan lantarki guda 12. Ku hada taron Zikiri (ambaton Allah عَزَّوَجَلَّ tare da salati ga Shugaban Halitta صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم) ko na rera baitoci na yabo ga Ma'aiki صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم a daren 12



www.dawateislami.net

ga watan Haihuwar Fiyayyen Halitta صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Sa'annan ku yi maraba da safiyar alkhairai (gabanin ketowar alfijir) cikin shauki mai hade da kwalla (hawaye) a yayin da kuke daga tutocin dake rike a hannuwanku tare da karanto salati da gaisuwa ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Idan da hali, za'a iya azumtar ranar 12 ga watan Rabi'ul Auwal domin Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya kasance yana azumtar dukkan ranakun litinin domin murnar haihuwarsa tare da nuna godiya ga Allah عَزَّوَجَلَّ.

Sayyiduna Qatadah رَضِیَ اللهُ عَنْهُ (Allah Ya yarda da shi) ya fada cewa, an tambayi Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم cewa meyasa Yake azumtar ranakun litinin. Sai Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya amsa da cewa, 'An haife ni wannan ranar kuma an fara saukar Min da wahayi a irin wannan ranar.' *(Sahih Muslim, pp. 591, Hadees 198)*

Mai tsokaci akan Sahih Bukhari, Sayyiduna Imam Qastalani رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه (Allah Ya mishi rahama) ya fada cewa: 'Daya daga cikin tabbataccen alfano na yin murnar Mauludin Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم shi ne samun kwanciyar rai da nutsuwa mai dorewa a gaba dayan shekarar tare da saurin samun biyan bukata. Allah عَزَّوَجَلَّ Ya kwaranyo rahama ga dukkan wanda ya raya dare daga cikin dararen Mauludi tamkar daren Idi.' *(Al-Mawahib-ul-Ladunniyyah, vol. 1, pp. 148)*

2. A yanzu haka a wannan zamani wasu sun kasance sukan yi amfani da samfuri na Ka'abah dauke da wasu samfuran

mutum mutumi na roba domin koyar da Dawafi ga maniyyata a wasu bangarori na duniya. Wanda kuma yin hakan ba daidai ba ne (aikin sabo ne). Domin gabanin zuwan Musulunci ya kasance akwai gumaka 360 a cikin dakin Ka'abah Mai Tsarki. Wanda bayan mamaye garin Makkah, Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya ciro dukkan wadannan gumaka daga Ka'abah. Wannan dalili ya sa bai kyautu a nuna koda samfuri na Ka'abah dake dauke da gumaka ba (samfuran mutum mutumi). Maimakon haka zai fi kyau a yi amfani da fulawowi (ko bishiyun) na roba. (Sai dai ya halarta amfani da iri iren wasu hotuna ko zanuka (a takarda, katako ko karfe da sauransu) dake nuni da taswirar dan Adam a gida ko masallaci da sauran wajaje idan har ya kasance cewa fuskar mutanen dake dawafin ba ta kasance abar bayyana karara a cikin taswirorin ba. Sai dai bai halarta amfani da irin wadannan taswirori ba muddin ya kasance ana iya ganin fuskokin mutanen dake cikin taswirorin karara yayin da suke tsaye akan kasa.

3. Bai halarta a sanya kofa dake dauke da adon hotuna ko taswirar dawisu da sauransu ba. Karanta wadannan Hadisai masu zuwa dake nuni da haramci dangane da hotunan abubuwa masu rai.

- Mala'ikun rahama ba sa shiga gidan da dauke a cikinsa akwai hoto ko kare. *(Sahih Bukhari, Littafi na 2, shafi na 409, Hadisi na 3322)*

- Duk wanda ya kirkiri hoton wani abu mai rai zai kasance cikin azabar Allah عَزَّوَجَلَّ matukar bai sanyawa wannan hoto rai ba, wanda kuma ba zai taba iya busa masa wannan rai ba (har abada). *(Sahih Bukhari, littafi na 2, shafi na 51, Hadisi na 42)*

4. A kan samu wasu mutane dake kunna kide kade da sunan murnar Mauludin Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. Aikata hakan ya kasance aikin sabo ne ta fuskar shari'ah. Wadannan Hadisai masu zuwa na Abin So Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم suke tabbatar da haramcin wannan aiki na kide kade.

- 'Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Ya fada cewa: 'An umarce Ni na karya (lalata) ganga da sarewa.' *(Firdaus-ul-Akhbar, littafi na 1, shafi na 483, Hadisi na 1612)*

- Sayyiduna Dahaak رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه (Allah Madaukaki Ya Rahamshe shi) ya rawaito cewa, kide kide yana lalata zuciya tare da janyo fishin Allah عَزَّوَجَلَّ. *(Tafsirat-e-Ahmadiyyah, shafi na 603)*

5. Za ka iya kunna faya fayan kasidodin bege amma wajibi a kiyaye lokutan kiran sallah da kuma tada sallah. A kuma tabbata cewa sautin kasidodin bai damu marasa lafiya ba ko mutanen dake bukatar yin barci ko kuma wadanda ke gudanar da wasu nau'ikan ibadu (kamar karatun Al-Qur'ani da Sallah). Kada ka kunna kowane irin faifai dake dauke da kasidar da muryar mace ke fitowa a cikin shi.

6. Bai halarta ba ga wani ya kawata tituna ko hanyoyi da

makamantan su ko kuma ya sanya tutoci ta yanda za su haifar da damuwa ko cutarwa ga masu wucewa a kafa ko a abin haqwa.

7. Matan dake fitowa daga gidajensu ba tare da sanya lullubi (hijabi) ba, domin kallon walkiyar haske (da makamancin haka) na aikata aikin haramun dake cike da rashin kunya tsababa. Koda ma dai ace sun, aikata hakan ne yayin da suke sanye da hijabin, hakika dunbin ukubar da aka tanada a cikin cakudedeniyar maza da mata na da matukar ban tsoro. Dadin dadawa, ba ya hallata a yi amfani da haramtacciyar hanyar wutar lantarki kamar dai ta hanyar jayo wuta ba bisa ka'ida ba. Sabida haka ka tabbata ka samu izini kuma ka biya kudin wutar lantarkin da za a yi amfani da ita.

8. Yayin da ka ke cikin tawagar Mauludi yana da kyau ka kasance a cikin yanayin tsarki na alwala har iya tsahon lokacin da ba zai gagara ba. Sannan ka tabbata ka kasance daya daga cikin masu halartar sallolin jam'i. Domin hadimai kuma mabiyan Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم bai kamata su zamo daga cikin masu rasa salar Jam'i ba.

9. Mu guji shigowa da amalanke na dawakai ko rakuma cikin tawagar, ganin cewa fitsari ko turosonsu kan iya bata tufafin masu wannan hidima da mahalarta wannan Mauludi.

10. Yana da kyau matuka ka kokarta iya iyawarka wajen ganin ka rarraba kananan littafai, takardu tare da faya fayan VCDs ko DVDs (bidiyo) dake dauke da sakunan maganganun



www.dawateislami.net

sunnah masu kayatarwa da Maktaba-tul-Madinah ta tanadar. Kuma a hada da rarraba yayan itatuwa da kayan makulashe (kayan ciye ciye) tare da tabbatarwa cewa an ba da su a hannun mahalarta Mauludin maimakon jefawa gare su, domin a mafi yawancin lokuta a kan samu cewa an wulakanta yayan itatuwa da sauran abubuwa ta hanyar take su da kafafuwa yayin da aka jefa su a kasa.

11. Rera baitoci na batanci ko cin zarafi ka iya haifar da wani mummunan yanayi abin ki wanda hakan zai iya kasancewa tamkar yin zagon kasa ne ga wnnan ayari na Mauludi abin girmamwa da soyuwa. Zaman lafiyarka ya ta'allaka ne da kasancewar ka cikin nutsuwa tare da kwanciyar hankali.

12. Kada ka taba yarda zuciyarka ta sosu ko ta harzuka ko kuma ka yi kokarin maida martani koda kuwa zai kasance cewa an samu saukar ruwan wasu duwatsu ne daga wasu masu nufin yin zagon kasa ga wannan taron. Domin kuwa aikata hakan zai kawo tsaiko da damuwa a cikin ayarin, wanda kuma tayu ma hakan shi ne ainihin manufar makiyin wannan taro da ya sa har ya kai ga aikata wannan mummunan aiki na jifa ga mahalarta taron.

*Ghunchay chatkhay phool mahkay her taraf aayi bahaar*

*Ho gayi Subh-e-Baharan Eid-e-Milad-un-Nabi*

*(Wasail-e-Bakhshish, pp. 465)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Wasikar Attar akan Murnar Bikin Mauludi

(Majalisin Madani ya bukaci da a sabunta karanta wannan wasika kowace shekara a matsayin tunatarwa a cikin taron satin karshe na ko'ina da ina da aka yiwa lakabi da taron Safara-ul-Muzaffar. Yan'uwa musulmi maza da mata na iya karanta wannan wasika ta sigar da suka so).

بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ Sag-e-Madinah Muhammad Ilyas Attar Qadiri Razavi (Allah Ya yi ma sa gafara) yana mai sallama (gaisuwa) da dukkan zuciyarsa zuwa ga dukkan masu hidima ga Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم a lokutan murnar bikin Mauludin Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

اَلسَّلَامُ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَةُ اللّٰهِ وَبَرَكَاتُهٗ

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ عَلٰى كُلِّ حَالٍ

*Tum bhi ker kay un ka charcha apnay dil chamkao*
*Aoonchay mayn aooncha Nabi ka jhanda ghar ghar mayn lahrao*

*Yana faranta zuciyarka yabo ga Annabi mafi girman Abin kauna*
*Tare da kafa tutocin Annabi a dukkanin gidaje*

1. A ba da wannan sanarwa a daren farko na watan Rabi'ul Auwal sau uku a dukkan masallatai:

   *'Barka barka ga dukkan yan'uwa Musulmi maza da mata!*
   *Da shigowar watan Rabi'ul Auwal watan haske!.'*

*Rabi'-un-Noor ummidaun ki dunya sath lay aaya*
*Du'aon ki qabuliyyat ko hathaun hath lay aaya*

*Lokacin sanya rai ya gabato a cikin watan Rabi'ul Auwal*
*Dukkan addu'o'i za su kasance amsassu nan ba da dadewa ba*

2. Mazan dake aske gemunsu ko rage shi kasa da tsayin da aka shardanta (wato kasa da tsahon kamu daya), suna aikata sabo ne da aikata hakan. Ga yan'uwa mata Musulmi da basu sanya hijabi, tabbas shima yin hakan aikata sabo ne mai girma. Domin samun cin nasarar taron Mauludi a watan Rabi'ul Auwal, an bukaci yan'uwa Musulmi maza da kullatar niyyar ajje gemu na din din din mai tsahon akalla kamu daya yayin da su kuma yan'uwa Musulmi mata ake bukatar su kulla niyyar amfani da hijabi (tufafi da shari'ah ta wajabta musu yayin fita cikin mazan da ba muharramansu ba). Da son samu ne zai fi kyau idan yan'uwa mata za su lazimci sanya tufafi irin wanda majalisin Madani ya ambata a matsayin tufa da majalisin ya aminta da ita wadda ta kasance ita ce, dogon hijabi dake rufe dukkanin sassan jikin mace tun daga kai har zuwa kafafunta, kuma wanda baya bayyana siffa ta yanayin kirar jikinta, ma'ana dai tufafi da ba mai matse jiki ba kuma ba shara shara ba. (Ga dukkan mutumin da yake aske gemu ko rage shi kasa da kamu guda (daya) ko kuma matar da bata sanya hijabi da sha'riah ta aminta da shi, su sani cewa sun kasance ne cikin aikata sabo kuma ya wajaba a gare su da su tuba cikin gaggawa su bar aikata wadannan aiyyuka na sabo).

*Jhuk gaya Ka'bah sabhi but munh kay bal aundhay giray*
*Dab-dabah aamad ka tha,* اَهْلًا وَّ سَهْلًا مَرْحَبًا



www.dawateislami.net

*Dakin Ka'abah ya jirkita, dukkan gumakan suka hantsula, Maraba! Maraba!*

*(Wasail-e-Bakhshish, shafi na 257)*

3. Wata babbar hanyan madani ta cimma burinta na kafuwar ayyukan sunnah da sauran ayyukan alkhairai ita ce tabbatarwa cewa dukkanin hadimai (Yan'uwa musulmi maza da mata) ga Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم sun daura niyyar gudanar da Fikr-e-Madinah (Tafsirin Ayoyi Al-Qur'ani Mai Girma a duk bayan sallar Asubahi) a kowace safiya, tare da cikewa a dan karamin littafi na Madani da aka yiwa lakabi da suna In'amaat, wanda kuma ake mika shi izuwa ga mai karba a dukkan karshen wata. Ku daga hannuwanku اِنْ شَآءَاللّٰه (cikin yardar Allah) yayin yin addu'a.

*Badliyan rahmat ki cha`een boondiyan rahmat ki aa`een*
*Ab muradayn dil ki pa`een aamad-e-Shah-e-Arab hay*

*Hadari dauke da Yayyafin alkhairai ya hado*
*Yanzu yanzu buruka za su cika, Maraba Maraba!*

*(Qabalah-e-Bakhshish, pp. 184)*

4. Dukkan hadimai ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم wadanda suka hada da Nigran (masu lura da sashe) da kuma Zimmahdar (jagorori) za su dinga yin tafiya a cikin tawagar Madani Qafilah (sashen tafiye tafiye) ta a kallah tsahon kwanki uku musamman a wannan watan mai albarka. Yan'uwa



www.dawateislami.net

musulmi mata kuma za su dinga isar da sakonnin Faizan-e-Sunnat (shashen dake kula da yada sunnah) har na tsahon kwanaki talatin a gidajensu (Wannan zai kasance ne kawai tsakanin mata da muharramansu) sannan kuma yana da kyau su kulla niyyar cigaba da gudanar da wannan aikin alkhairi koda bayan wucewar watan rabi'ul Auwal.

*Lootnay rahmatayn Qafilay mayn chalo*
*Seekhnay Sunnatayn Qafilay mayn chalo*

*Domin rabauta da alkhairai, yi tafiya cikin Qafilah (ayarin Madani)*
*Domin koyon sunnah, shiga tafiyar Qafilah (ayarin Madani)*
*(Wasail-e-Bakhshish, shafi na 611)*

5. Kafa tutoci guda 12 ko kuma a kalla guda daya a Masallaci, gida, shago, wajen aiki da dai sauransu tun daga ranar shigar watan Mauludi har izuwa fitarsa. Ku siyi wasu tutoci domin sanya su a jikin ababan hawa kamar su doguwar motar bos (bus), kananan motocin daukar kaya rufaffu (wagons), manyan motoci na daukar kaya (trucks), kwandunan tura kaya (trolleys), kananan motocin haya (taxis), ababan hawa masu kafa uku (kaman su Keke Napep), amalanke na dawakai (horse-carriage) da dai sauransu. Sannan ku sanya tuta a babur mai kafa biyu ko sukuta, da kananan motoci na gida.

(اِنْ شَآءَاللّٰه Ya yarda) gaba daya birnin zai cika da walwala yayin da koraren tutoci za su yi ta jujjuyawa. A mafi



www.dawateislami.net

yawancin lokuta wasu masu manyan ababan hawa (na daukar kaya) kan sanya manyan hotunan halittu masu rai ko kuma rubutun wasu baitoci marasa kyau a bayan ababan hawansu (wanda kuma ba daidai bane aikata hakan).

Ina ma dai ace wannan baiti mai zuwa kamar haka 'Ina kaunar Dawatul Islami' shi ne zai kasance a rubuce karara a bayan wadannan manyan motoci na daukar kaya (trucks), dogayen motoci na haya (bus), kananan motocin daukan kaya rufaffu (wagons), ababan hawa masu kafa uku (rickshaws), kananan motocin haya (taxis) dana gida (cars) da dai sauransu. Yi kokari ka ba da gudunmawa ta wannan bangare wajen ganin cewa ka sadu da masu wadannan ababan hawa kama daga kan motocin hawa izuwa na daukar kaya tare da gamsar dasu game da alfanon wannan aiki. Tabbas kuwa dana kasance daya daga cikin masu yi maka addu'o'I na alkhairi.

## Gargadi

Yayin da tutar ke dauke da rubutu ko taswira ta kayayyakin amfani na Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم masu albarka (kamar su hoton kasan takalmin Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم), ka tabbata cewa ba a yaga ko kuma jefar da wannan tuta a kasa ba. Dadin dadawa kuma a tabbata cewa, an cire ta (tutar) daga wannan abin hawa da zarar watan Mauludi ya kare (domin ajje ta a waje mai tsafta). Idan kuma kana ganin cewa akwai alamu koda kadan na yuwuwar wulakantar wannan tuta, toh zai fi kyau kawai a yi

amfani da korayen tutuci da basa dauke da irin wadannan tsarkakan kalamai ko hotuna.

(Sag-e-Madinah ya yi amfani da koriyar tuta wadda ba ta dauke da rubutu ko hoto a gidansa da ake kira *Bayt-ul-Fana* [Gidan Daraja]).

*Nabi ka jhanda lay ker niklo dunya mayn cha jao*
*Nabi ka jhanda aman ka jhanda ghar ghar mayn lahrao*

*Jagoranci dukkan duniyya dauke da tutar Annabi*
*Ita tutar zaman lafiya ce; don haka ku kada wannan tuta mai girma a kowane gida*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب    صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

6. Haskaka gidanka da zarurrika guda 12 na haske ko kuma da akalla gulab na lanntarki guda 12; sannan ku sanya fitulu na kawatarwa a mahallinku da masallaci (amma dai ka sani cewa ba daidai bane yin amfani da haramtacciyar wutar lantarki ko kuma ta hanyar sabawa ka'ida, dan haka a tabbata an bi ka'idar kamfanin dake ba da hasken wutar lantarki kuma an biya kudin wutar lantarkin da aka yi amfani da ita). Ku kawata dukkan muhallinku da ado ta hanyar amfani da korayen tutoci, kyallaye da kwayayen wutar lantarki masu haske. Kafa manyan tutoci (masu akalla tsahon mitoci 12) a saman rufin gidajenku da



www.dawateislami.net

masallatai da kuma ainihin cikin farfajiyoyinsu da dai sauran wurare ta yanda ba za su tare ko haifar da damuwa ba a hanyoyi na zirga zirgar jama'a na kasa ko na kan ababan hawa, misali kamar wajen haifar da cunkuso da dai sauransu. A takaice a tabbata dai ba'a shiga hakkin jama'a ba. Kada a kafa tutoci a tsakiyar tituna domin wannan zai haifar da tsaiko ga tafiye tafiyen ababan hawa. Kada a kawata hanyoyi na cikin gari da sauransu ta hanyar da zai jawo tsukewar hanya tare da shiga hakkin al'ummah.

*Aik mashriq, aik maghrib, aik baam-e-Ka'bah per*
*Nasb parcham ho gaya,* اَهْلًا وَّ سَهْلًا مَرْحَبًا

*An kafa tutoci, daya a Gabas, daya a Yamma dayar kuma a saman rufin Ka'abah domin maraba da zuwan Annabi Abin So*

*(Wasail-e-Bakhshish, pp. 453)*

7. Kowane dan'uwa Musulmi ya raba kananan littafai ko mujallu (takardu) mabambanta da Maktaba-tul-Madinah ta wallafa daidai gwargwado ko kuma dai wanda bai gaza na adadin kudi na akalla 12 PKR (Pakistani Rupee) na kudin Pakistan ba, wanda a yanzu haka ke daidai da kwatankwacin naira 28 da rabi na kudin Nigeria. Kuma a tabbata cewa an raba su a tsakanin mahalarta ayarin (taron) Mauludi. Suma dai yan'uwa musulmi mata yana

da kyau su kasance daga cikin masu irin wannan rabo na wadannan littafai ko mujallu (takardu) dake dauke da sakonnin Majalisin Madani.

Hakanan kuma yana da kyau ku ba da gudunmawarku wajen kira izuwa aikin alkhairi ta hanyar ajje wadannan takardu a shagunanku da sauran wajaje domin raba su kyauta a cikin shekarar gaba dayanta. Sa'annan yana da kyau ku yi kokarin raba irin wadannan sakonni a tarukan aure, mutuwa da dai sauransu ko kuma ga masu kokarin nemawa wani mamaci lada (yin sadakatul jariya ga wani mamaci). Sannan kuma a rinjayar da sauran Musulmi wajen ganin cewa sumasun shiga sahun masu aikata irin wadannan ayyuka na alkhairai.

*Baant ker Madani rasaail Deen ko phaylaaiye*
*Ker kay razi Haq ko haqdar-e-jina ban jaaiye*

*Yada sunnah ta hanyar raba kananan littafan (mujallun) Madani*
*Nemi Aljannah tahanyar farantawa Allah (neman yardar Allah)*

8. Idan da hali ka siyi littafai 12 da aka lakawa suna 'Safiyar Alkhairai' da kuma mujallun (takardun) dake dauke da sakonnin sunnah, guda 112 ko a kalla guda 12, da aka yiwa lakabi da suna: 'Fitattun Nasarorin Madani guda 12 da suka samo asali daga gudanar da murnar Mauludin Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللّٰه عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم' wanda ya zo daga Maktaba-ul-Madinah. Sai ka bayar da su kyauta musamman ga shuwagabannin kungiyar da suka shirya



www.dawateislami.net

taron Mauludin. Raba 1200 PKR (2,828 NGN) ko kuma 112 PKR (264 NGN) idan babu halin ba da na farkon a cikin watan Rabi'ul Auwal ga wasu malaman Sunnah (baligai ne kadai za su iya aiwatar da wannan banda yara da sauransu). Sa'annan za ka iya kuma ba da wannan kudi ga Limam, Ladan ko kuma wani hadimi ga masallaci, wanda idan so samu ne sai ka kulla niyyar cigaba da aikata wannan kyakkyawan aiki a duk watan duniyya.

Mafi kyautuwa shi ne ba da wannan kudin ranar Juma'a sabida kasancewar cewa ladan ko wane aiki ya kan ninku (karu) da kashi 70 a ranar Juma'a.

اَلْحَمْدُ لِلّٰه (Mun godewa Allah عَزَّوَجَلَّ)! Faya fayan Bayanaat (dake dauke da bayanai akan maganganu masu kayatarwa na Sunnah) wadanda suka fito daga hannun wannan majalisi na Makhtaba-tul-Madinah sun taka gagarumar rawa wajen kyautata ko canja rayuwar mutane da dama (izuwa rayuwa ta sunnah). Watakil koda wasu a cikinku sun samu kansu ne cikin wannan majalisi na Dawat-e-Islami sakamakon sauraron wasu daga cikin wadannan faya fayan dake dauke da bayanan sunnah masu kayatarwa. Rarraba wadannan faya fayai na VCDs ko DVDs ga al'ummah ba karamin aiki bane ta fuskar daukaka addinin Musulunci kuma hanya ce sassauka ta tara dumbin lada mai tarin yawa. Sabida haka idan da hali yana da kyau ka siyar da 12 na irin wadannan faya fayai

na VCDs ko DVDs dake dauke da kayatattun sakonnin sunnah a kowane sati ko kuma a kalla kowane wata. Masu hali daga cikin yan'uwa Musulmi za su iya yin wannan aiki na samun lada kyauta. Domin murnar bikin Mauludi, sai ka raba wadannan faya fayai iyakacin iyawar ka, ko kaima ka kasance daya daga cikin masu rabauta da dumbin ladan dake cikin aikin yada Sunnah.

Bayar da kyautukan littafai ko faya fayan VCDs/DVDs a tarukan aure hade da katin goron gayyata. Sannan ka sauya al'adar nan ta ba da katin gaishe gaishe a yayin Idi (ko biki) da raba wadannan littafai da sauran su a madadin wancan (katin gaishe gaishen), tayan da kudin da ka kashe zai yi amfani a wajen daukaka Sunnah. Mutane kan aikomin da katinan gaishe gaishe masu tsada yayin bikin Idi wanda yin hakan na sanya min damuwa maimakon ace ya faranta mini. Yanzu mutun ba ya kashe kudin da ya sha wahala ya nema da kyar ba, wajen daukaka addini maimakon kashe su ta hanyar siyan katunan gaishe gaishe na Idi masu tsada ba! Bayan haka ma kuma wannan garin hoda na jikin katunan gaishe gaishen dake sanya shi wannan kyalkyalin, kan haifar da gagarumar damuwa.

*Un kay dar pay palnay wala apna aap jawab*
*Koi Ghareeb Nawaz to koi Daata lagta hay*

*Wadanda suka rabauta da Annabi hakika babu ya su*
*Wani ka iya zama talaka amma mai kirki ga yawan kyauyta*

9. A manyan birane kowane 'Alaqa'ee Nigran (mai kula na shashe) zai hada taruka masu kayatarwa na Sunnah a masallatai daban daban a kwanaki 12 na farko dake cikin watan Rabi'ul Auwal (Yan'uwa mata musulmi dake da alhakin aiwatarwa za su yi nasu tarukan a gidajensu). Idan da yiwuwa, kowane mahalarcin irin wadannan tarukan ya kasanceyana halartar kowane irin daya daga cikinsu a cikin wannan wata na Rabi'ul Auwal yayin da yakerike da korayen tutoci.

*Lab par Na'at-e-Rasool-e-Akram hathaun mayn parcham*
*Diwanah Sarkar ka kitna piyara lagta hay*

*Hadiman Annabi dake rera baituka rike da korayen tutoci, akwai matukar kayatar da idanuwa*

10. A yi wanka a yammacin ranar 11 ko daren 12 ga watan Rabi'ul Auwal. Idan zai yiwu ka siyi komi sabo, misali, fararen kaya, rawani, dankwali ko makamancin sa, hula, mayafi ko makamancinsa, asuwaki, hankici, takalmi, carbi, turare, agogon hannu, alkalami (biro), Qafilah pad da sauransu, duk dai domin halartar wannan biki na Idin Idodi. (Haka yan'uwa Musulmi mata ma, na da kyau su siyi sababbin kayyayaki daidai da bukatunsu da kuma zurfin aljihunansu).

*Aayi nayi hukumat sikkah naya chalay ga*
*'Aalam nay rang badla subh-e-shab-e-wiladat*

*Sabon kudi za'a yo tunda sabon zamani ya fara*
*Da bayyanar safiyar alkhairai sabuwar doka (rayuwa) ta bullo*

*(Zauq-e-Na'at, shafi na 67)*

11. Ku karar da daren 12 ga wannan watan a wajen taron Zikiri da baitoci sannan ku yi maraba da 'Safiyar alkhairai' yayin ketowar alfijir, ta hanyar nuna murna mai sanya idanuwa kwalla, tare da daga tutocinku yayin da ku ke karanto Salati da Gaisuwa. Sa'annan bayan gudanar da sallar asuba a wannan dare sai ku yi musabaha da juna tare da taya juna murna a wannan gawurtaccen taron Idi (ta bikin Mauludi) tare da cigaba da kasancewa a cikin wannan hali na murna da farin ciki tsahon wannan rana mai albarka. Sa'annan kuma a cigaba da kokarin taya juna murna a cikin wannan rana ta Idi.

*Eid-e-Milad-un-Nabi to Eid ki bhi Eid hay*
*Bil-yaqeen hay Eid-e-Eidaan Eid-e-Milad-un-Nabi*

*Shakka babu Idin Mauludin Nabi ita ce mafi girman idi ga dukkan idodi*

*(Wasail-e-Bakhshish, shafi na 465)*

12. Annabinmu Tsakakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya kasance yana azumtar ranakun litinin domin nuna murnar haihuwar Shi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم. yana da matukar muhimmanci kaima ka sanya a zuciyarka cewa kaima za ka azumci ranar 12 ga watan Rabi'ul Auwal tare da kasancewa cikin ayarin Madani wanda ma'abota cikinta ke hallara a wannan rana hannayensu rike da korayen tutoci. Sannan kuma a yi kokari a wanzu cikin yanayi na tsarkin alwala gwargwadon iyakacin tsahon iyawar mutun. Bayan haka kuma ka zamanto cikin masu rera kasidodi ko baitocin

yabo tare da yin salati da gaisuwa ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم tare da yin tafiya cikin taku mai kawatarwa sa'annan kuma ka kasance mai yin kasa kasa da ganinka (cikin kaskan da kai) yayin gudanarda wannan kewaye. Kada ka ba da kofa ta suka ga wannan zageye na Mauludi ta hanyar aikata kowane irin abu da ka iya zubar da kimarka ko ta wannan ayari.

*Rabi'-ul-Awwal Ahl-e-Sunnat tujh per kyun na haun qurban*
*Kay tayri Barhween tareekh woh Jan-e-Qamar aaya*

*Rabi'ul-Auwal, Mai zai hana Mabiyan-Sunnah sadaukar da rayukansu domin tabbatar da tsafta (da martabar) wannan lokaci, domin kuwa Annabi Mafi Girman Abin So ya iso ne ranar 12 gare shi (watan)!*

*(Qabalah-e-Bakhshish, pp. 37)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Niyya Akan Gudanarda Bikin Mauludi

Haidisin da aka gabatar a farkon Littafin Sahih Bukhari shi ne wanda ke dauke da lafazi kamar haka: اِنَّمَا الْاَعْمَالُ بِالنِّيَّاتِ (dukkan ayyuka saida niyya), 'ma'ana darajar ayyuka ko ladansu ya ta'allaka ne akan niyoyi (na gudanar da su).' *(Sahih Bukhari, littafi na 1, shafi na 5)*

Ka tuna cewa duk sanda ka aikata wani abu na alkhairi, dole sai

ka kullaci niyyar neman lada daga Allah عَزَّوَجَلَّ akan wannan aiki da za ka aikata. Idan ba haka ba kuwa sai ka kare ba tare da samun koda digo na lada daga aiwatar da wannan aiki da ka aikata ba. Haka kazalika ya zama wajibi a kudirci niyyar samun lada yayin murnar bikin Mauludi. Tabbas yayin da ka kulla niyyar neman lada daga wannan aiki na gudanar da bikin Mauludi, toh kuwa ko shakka babu aikin zai zamo ya yi daidai da aiki irin na Shari'ah amma dai duk da haka dole ya zamanto an aikata shi da tsarkakakkiyar niyya ta gaskiya. Wanda duk ya gudanar da bikin Mauludi da nufin nuna isa, ko kuma ya yi amfani da haramtacciyar wutar lantarki, ko ya tilastawa mutane ba da kudi ko gudunmawa (ba bisa son ransu ba), ko kuma ya taba hakkin al'umma wajen shiryawa ko ko gudanar da taron, kaman dai ta hanyar kunnan baitoci a manyan na'urorin sauti (sifiku) da gangan, tare da sanin cewa zai takura ko cutar da marasa lafiya, jarirai da ake shayarwa, ko mutane dake bacci, toh tabbas niyyarsa ta samun lada za ta baci. Maimakon ma ya samu lada sai dai ya kare da tulin zunubin sabo da ya aikata. Yana da kyau mu fahimci cewa yawan ladan da za ka samu ya danganta ne da iya matsayin kyawun niyyarka (muddin dai ba ka aikata aikin sabo ba a yayin gudanar da ayyukanka). Wannan shi ya sanya muma mu ka zauna mu ka zakulo tare da gabatar da wadannan kyawawan niyyoyi guda 18 da duk wani mai shirin gabatar da bikin Mauludi ya kamata ya sanya a cikin niyyoyinsa domin ya rabauta da dumbin alkhairan dake tattare da su. Duk da dai wannan ba yana nufin wai su kenan ba domin Malami dake da



www.dawateislami.net

sani a wannan fanni na niyya ka iya zakulo wasu karin niyyoyin daban gwargwadon yanayi irin naka. Wadannan Niyyoyi guda 18 sune kamar haka:

## Niyyoyi 18 Domin Gudanar da Murnar Mauljudi

1. Zan bayyanawa al'umma babbar rahamar Allah عَزَّوَجَلَّ ne, sabida haka ya zama wajibi na tsaya a bisa umarni da hani na Al-Qur'ani Mai Tsarki:

وَاَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ﴿١١﴾

*Kuma amma ni'imar Ubangijinka, sai ka fada (domin godiya)*

*[Kanz-ul-Inan (Fassarar Al-Quran)] (Sura ta 93, Suratul Duha, Aya ta 11)*

2. Zan Kawata taron Mauludi da fitilu masu haske da walkiya domin na sami yardar Allah عَزَّوَجَلَّ.
3. Zan kafa tutoci a kokari koyi da aikin Sayyiduna Jibril (Tsira da aminci ya tabbata a gare shi) Wanda ya kafa tutoci 3 a ranar haihuwar Annabi (Abin So) صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.
4. Zan kafa korayen tutoci domin Hasumiyar Masallacin Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ta kasance kuriya ce.
5. Zan nuna girma da martabar Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ga wadanda ba su kasance Musulmai ba, ta hanyar gabatar da bikin Mauludi (Yayin da za su ga walwalin haske da korayen tutoci, tabbas wadanda ba Musulmai ba za su kayatu kuma za su tabbata cewa Musulmai suna son AnnabinSu صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم matukar so da kauna).

6. Zan bakantawa Shaidan ta hanyar gudanar da bikin Mauludina cikin shauki da annashuwa.
7. Bayan kawa ta zahiri, zan kawata zuciyata (ta hanyar cika ta da alkhairai) tare da neman gafara akan ayyukan sabo dana aikata da kuma tuba (wajen yin niyyar barin aikata su har abada).
8. Zan halarci taron Mauludi a daren 12 ga wata (Rabi'ul Auwal)
9. Zan shiga cikin tawagar (ayarin) Mauludi a ranar 12 ga watan Rabi'ul Auwal kuma zan wanzu cikin (zikiri) Ambaton Allah عَزَّوَجَلَّ da AnnabinSa صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Abin Kauna.
10. Zan sadu da manyan malaman addinin Musulunci da kuma
11. Bayin Allah عَزَّوَجَلَّ nagari (masu Tsoron Allah)
12. Zan ribaci tarin alkhairai masu dumbin yawa yayin kasancewata a cikin hadimai ga Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.
13. Zan nada rawani yayin da na ke cikin wannan ayari kuma
14. Zan kasance a cikin tsarki na alwala har iyakacin tsahon iyawa ta
15. Zan yi sallolina a cikin jam'i tare da sauran jama'a a masallaci yayin gudanar da wanna taro.
16. Zan yi iyakacin iyawata wajen raba littafai, takardu da faya fayai na VCDs ko DVDs dake dauke da sakonnin Sunnah masu kayatarwa wadanda Maktaba-tul-Madinah ta wallafa, yayin gudanar da wannan taro na Mauludi da zagaye a cikin ayari.

17. Yayin ba da gudunmawa ta kashin kai zan yi kokarin ganin na ja ra'ayin yan'uwa guda 12 dan su shigo su yi tafiya cikin ayarin Madani.
18. Zan dauwama cikin karanta Salati, gaisuwa da baitoci iya iyawata yayin zagayen tare da aiwatar da Qufl-e-Madinah na harshe da idanuwa (Kame gani da harshe).

Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Muna rokon Ka, da Ka bamu ikon gudanar da bukukuwan murnar haihuwar AnnabinKa Abin So صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم da dukkan zukatanmu Ka agaje mu da kyawawan niyyoyi kuma Ka rabauta mu da shiga Aljannah ba tare da tuhuma ba domin albakacin wannan Mauludi na haihuwar AnnabinKa Abin So صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*Bakhsh day ham ko Ilahi! Bahr-e-Milad-un-Nabi*
*Naamah-e-a'maal 'isyan say mayra bharpoor hay*

*Ya Mai Cikakken Iko (Allah), yafe min albarkacin Mauludi*
*Duk da cewa littafina ya kasance cike makil da tarin zunubai*

*(Wasail-e-Bakhshish, pp. 477)*

اٰمِين بِجَاهِ خَاتَمِ النَّبِيّٖن صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد



Muhammad Ilyas Attar Qadiri
17 Ga Watan Safar-ul-Muzaffar
(Safar), 1427 AH



www.dawateislami.net

الحمد للّٰه رب العٰلمین والصلوة والسلام علی سید المرسلین اما بعد فاعوذ باللّٰه من الشیطٰن الرجیم بسم اللّٰه الرحمٰن الرحیم

## Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَآلِهٖ وَسَلَّم Na Farin ciki da masu Nuna Farin Cikin HaihuwarSa

Wani malamin Addinin Musulunci ya fadi cewa ya ga Annabin talikai صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَآلِهٖ وَسَلَّم, Wanda Ya kasance kwanciyar rai da nutsuwar ga zukatanmu, kuma mafi karamci da kyautayi (kirki), a cikin mafarkinshi har ya tambaye Shi da cewa, 'Ya Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَآلِهٖ وَسَلَّم, Ko Kana farin ciki da Musulmin dake nuna farin ciki da haihuwar Ka?' Annabi Tsarkakakke صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَآلِهٖ وَسَلَّم Ya amsa masa da cewa, 'Ina farin ciki da wanda ke farin ciki da Ni.'










Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagaran
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan
UAN: +92 21 111 25 26 92 | Ext: 7213
Web: www.maktabatulmadinah.com | E-mail: feedback@maktabatulmadinah.com